# FADAKARWA

## A kan: Sanin makamar kasuwanci

## Kashi na 2: Muhimman batutuwa a kan gudanar da al'ámuran shiga da fitar kudi a kasuwanci

**1. Kudaden dake shigowa**

Wannan sune kudaden da suka shigo sakamakon harkokin kasuwanci, kamar sayar da wasu kaya, ko kudin hayar gidaje, ko karin banki. Kudin da mutum ya samu ta hanyar da bata shafi kasuwancinsa ba suma kudin shiga ne. Misali, kudin da a ka ba mutum kyauta.

**2. Kudin da a ka batar/ kashe**

Watau kudin da suka fita daga hannun dan kasuwa domin sayen kaya ko biyan ladan aiki ko biyan kudin hayar shago ko biyan karin banki, da sauransu.

**3. Kadara**

Kadara a harkar kasuwanci ta kasu kashi-kashi, misali:

- Kadarorin da suke kayyadaddu , kamar kayan aiki, misali, kujeru da tebura da kuma abubuwan da a ke biya yau da kullum, kamar kudin haya, wuta da kudin leburori.
- Akwai kuma kadarar da sukan farune daidai da darajar da lokaci ko bukata kan canzasu, kamar hannun jarin wani kamfani, da a ka saya.

**4. Riba**

Watau abin da ya ragu daga cinikinda akayi bayan an cire dukkan wahalhalu. Ya kamata a lura cewar ciniki daban, riba daban.

**5. Jari**

Za a iya kara karfin jari domin neman bunkasar kasuwa, misali idan a ka gyara shago domin jawo hankalin abokan ciniki ko, yin tallan kaya a rediyo ko, a kara kaya a shago. Za a iya neman bashi a banki domin kara karfin jari.

**6. Bashi**

Bashi wasu kudi ne da za a nema daga banki ko a hannun wani mutum da niyar biya bayan wani lokaci kayyadajje. Wasu lokutan a kan biya wani kari a bisa bashin da aka ci a matsayin ladan bashi. Za a iya neman bashi domin bunkasa jari. Idan jari ya bunkasa,

kasuwa zata inganta, kuma za a sami damar biyan bashi cikin sauki. Rashin biyan bashi laifi ne, kuma mai taurin bashi ba za a ba shi bashi ba nan gaba.

**7. Lamuni**

Wani lokaci dan kasuwa zai iya karbar kaya, wajen abokin ciniki da yarjejeniyar zai biya a wani lokaci a gaba.. Wannan ya na nufin zai biya a wani kayadajjen lokaci a gaba. Irin wannan tsari yana taimakawa manoma yadda zasu karbi kayan aikin gona lokacin da suke matukar bukatarsu, kuma babu kudi a hannunsu. Zasu biya wannan kudi bayan sun ci amfanin gona.

Amma ya wajaba dan kasuwa ya yi hattara wajen bayar da kaya ta hanyar lamuni, sabo da gudun kada ya bayar da abin da yafi karfin jarinsa. Karya yarjejeniyar lamuni laifi ne, kuma mai yin haka ba za'a lamunce shi ba.

8. **A lura, *bashi*** ya sha ban-ban da ***lamuni***. Bashi ya kunshi bayar da kudi domin sayen kaya, amma lamuni kayan za a baiwa mutum kai tsaye. Amma dai duk sun kunshi biya bayan wani lokaci, kuma zai iya zama sai an yi kari akan darajar abinda aka karba.